"Daddyyyyyy a wanan mansion ɗin zaka ajiyeta ita kaɗai bama damu ba, sabida baka sonmu wallahi na tsaneta kuma idan tazo dole tabar mana kai, i with not let her to take u away for us i hater her."
Tana gama faɗar haka ta juta tabar gurinshi, dafe goshinsa yayi ya bar falon,

Wasa gaske matan mai nasara suka shiga zuga Mufida, da ta buɗewa Ubanta wuta, dan kar ya aure.

Tun abin bai damunshi har yakai, kanshi yayi masifar zafi tun ba'a a fara komi ba, Sun taso shi a gaba da fitina, sai da ya kare ranar ya fito musu namijin duniyarshi.
"Daddy ka fasa kawo wancan banza da kake son aurowa."

Dake haka suka zugota ta faɗa mishi. Takaici da bakin ciki suka sashi, zare wayar chaji ya shiga tsula mata,ba kakkautawa sai da uwarta tazo da kanta ta kwaci yarta, tana mi kallon cikin idanunshi ita kanta sai da ta razana amma dan karfin hali tace.
"Dan zakayi aure sai akace ka kashe min Y'a."

Dago hargitsatsun idanunshi yayi ya kafa mata, dole yasa tayi baya, tsawon shekara goma sha biyar bata taɓa ganin fusatarshi sama da yau ba, fita tayi tabar mishi falon da Mufida, tun kafin su isa side din uwar tace.
"Ni ki sake ni, wallahi sai nasashi ya mata dukan da yayi min, kuma dole yakaimu can ɗin inda zai sakata."

Sosai Al'amarin Mufida yabawa balkisu haushi ta kifa mata mari ita ma, sannan ta tureta a gurin,

........
"Hakuri shine mafita hindu matukar kika ce zakiyi faɗa karshe idan giyar amarci ya kwaso shi ya sakeki kinga ai kin faɗi ba nauyi."

Shiru Hindu tayi tace.
"Hmmm yarinya karama ta haukata shi ya wucce."

Haka suka rabu da Hafsa zuciyarsu ba daɗi dan itama ɓoye nata take amma ba wai tana cikin jin daɗi bane.

****
A ɓangarenmu anata hidima, ba kama hannun yaro.

Ina kwance idanuna a rufe, sai ganin Yar budurwa nayi a kaina tashi nayi na zauna nace.
"Sannu da zuwa."
"Yawwa. Aunty Mom."
Sam sai naji sunan yayi min girma, murmushi tayi sannan tace.
"Baki ganeni ba ko? Nida Daddy muka zo, yana waje munzo da tela ne ki zaɓi style ɗin da kike so."
Duk sai na diririce na shiga ruɗu nace.
"Toh bari na kawo miki ruwa mana"

Fuskarta ɗauke da murmushi tace.
"Barshi kawai, muje."

Fita nayi na ɗiba mata ruwa na kai mata, kurɓa ɗaya tayi ta ajiye tace.
"Muje ko."

Fitowa nayi na kalli Umma nace.
"Hmm dama yazo ne, yace wai."

"Toh uwar shiririta mi muka ce miki bismillah kuje." Inji Mams knn,
Fitar da nikk'af ɗina nayi na ɗaura akan fuskana, zarewa Yarinyar tayi cike da mamaki tace.
"Lallai gurin Daddyn nawa zaki da nikk'af ai wannan abin an daina show ɗinshi, muje haka kuma baki tambayi sunana ba, kinga ni dake na damu sai da nace ya kawoni gurinki."

"Kiyi hakuri hmm bansa ba fita haka ba."
"Toh yayi....."

Kuyi hkr Daga yau zuwa friday zakuna hakuri dani....

[8/25, 2:59 PM] Real Mai Dambu: 🌹🌹🍀
*MATAR SO*

🌷🌷🌻

*MAI_DAMBU*
*Wattpad:Mai_Dambu.*
*HAZAKA WRITER'S ASSO*
(HWA)

Da sunan Allah Mai Rahama Mai Jinkai....

Dedicater To Hafsat Abubakar💋

_Wannan buk ɗin hakk'in masu shine idan kinsan baki saya ba karki karanta, mai fitarwa kuma ki duba girman Alkawarin da kika ɗauka na cewa bazaki fitar ba, tunda nace idan kinsan zaki saya ki fitar na Yafe ba sai kin saya ba_

*BOOK 1👈*

*Page....14*

"Allah ki ajiye nik'af ɗin nan sai kace ba Yar kaduna ba,muje haka mana."

Mai da shi nayi cikin hijab ɗina nabi bayanta kamar rak'umi da akala,

har gurin motarshi muka isa, suna tsaye shida wani matashi da alamun shine telan, kaina a kasa na gaidasu, telan ne ya amsa dan ko kallo ban isheshi ba, mika min album telan yayi yace.
"Madam gashi ki zaɓe kalar da kike so."

Karɓa nayi jikina na rawa, ina satar kallon Mai nasara wanda ya juyar da fuskarshi wani guri daban, jan hannun Huda nayi muka koma gefe nan tayita nuna min, wasu style ni duk sai naji kayan sun bani kunya, sabida akasarinsu masu buɗaɗɗiyar kirjine ni kuma ina kunya sosai, da muka gama dubawa na mika mata album ɗin nace.
"Wai duk wannan na meye."

Kallona tayi cike da mamaki sannan tace.
"Baki san za'ayi dinner bane."

"Dinner gaskiya bazanje ba! Ki faɗa mishi asuke dinner dani."

Shiru tayi, tabar gurina wajenshi taje tace.
"Daddy wai ita, bata son dinner ko za'a fasane sai a maidashi liyaffa, tunda haka ranta keso."

D'ago kanshi yayi, akayi dace nima na ɗago muka zubawa juna ido, kauda kanshi yayi yana mi

taɓe baki ya kalli tela yace.
"Ok kaji wai haka bai mata ba, zamu iya tafiya."

Baya telan ya shiga huda ta shiga gaba, takowa yayi har gabana kaman ance na ɗaga kaina sai a fuskarshi, sunkuyar da kai nayi kasa jikina ya fara ɗaukar rawa, kallona yake daga sama har k'asa kamar wanda akasahi maganar dole yace.
"Kina da zaɓin abinda zaki yi ne? Dan matukar na tafi babu abinda zai dawo dani."

Tsabar na dirirince ban taɓa tsayuwa haka ba, sai gabaki ɗaya jikina ya ɗauki rawa bansan ya akayi ba na fashe da kuka, ina ja da baya.
Mamakin halina yake, yanda kuka bai bani wahala, kallon yanda nake ja da baya har na kusan faɗawa lambatu, kawai sai naji an finciko ni bazata na faɗa kanshi tare da cusa kaina a kirjinshi.

Runtsa idanunshi yayi hannunshi ɗaya na bayana ɗaya hannun ya dunkule shi kamar zau zabga naushi, saukar zafaffan kwalla daga idanuwana zuwa kan chest ɗinshi yasa shi ɗagoni ya ture ni sannan ya juya motarshi, yanda ya ture ni kuwa zuɓewa nayi a kasa, tare da sake kuka haka yaja motar suka tafi, yana lura da yanda huda ta kafeshi da ido.

Dakyar na mike na shiga gida, abin mamaki ina zare hijab ɗina Aunty gausiya tace.
"A ina kika samu, turare mai karfi haka a tsorace na sunsuna hijab ɗin naji ai turaren mai nasara ne, ai kuwa nayi wurgi da hijab ɗin tare da zuba gwiwa na kasa nace.
"Don Allah ki rufa asiri wallahi tsausayine ya rufta dani ya taimake ni shine, jikinmu ya haɗu da juna amma ni ba Yar iska bace."
Dariya tayi tace.
" Ni ban tambayeki ba, kamshin ne yayi min daɗi da zaki min dogon turanci."

Tsabar ganin yanda na ruɗe dariya tayita min.

****

Tunda suka bar kofar gidan mu yake satar kallon inda kwalla na ya jika mishi, yanayin da abin ya faru yasashi faɗawa wani yanayi  na daban, sauke drvn yayi ya wuccw gida da huda..

****

Sati biyu ya rage ayi bikin muna zaune da dare sai ga Rahilah tazo, tsiya muka shiga mata tana dariya,

Dakin iyayenmu tashiga suka gaisa sannan ta faɗa musu abinda ya kawota, shiru Malam yayi kafin yace.
"Da fatan ba irin wanda akayi na watsewa zaku yi ba."

"A'a malam cikin shiga mutunci da kima zamuyi, kuma za'a kawo muku hotonan ma."

"Shi knn, kuje."
Godiya tayi sannan tazo ta samu muka fita, sai da muka fita har mun shiga motar Mijinta sannan take faɗa mana abinda zamuyi, aikuwa nace bansan da haka ba,

Share ni tayi muka tafi.

A can muka sami Mai nasara da Ahmad wani ɗaki aka ware mana, muka shiga aka shirya mu, ba gurin ɗaukar hoto bane gidan saukar bakinsune anan muka sami mai kwalliyar,

Bayan wasu lokuta muka fito aka fara ɗaukar hotonmu, munyi mu uku munyi sai wanda mukayi da mazajenmu kowa da kalar kayanshi, dake bana jure shagali haka dakyar aka gama abubuwan dani.

Duk wanan bidirin da muke ko kallon juna bamayi, asalima yakan ajiye gefe guda.

Sai da aka kusan gamawa yace.
"Ku bani guri a mana na karshe."
A birkice na shiga kallonshi komawa gefe yayi sukayi magana da mi ɗaukar hoton, sannan ya dawo gurina harara na yayi yace.
"Sai nace ki tashi."
Mikewa nayi ina daidaita zaman gyalena, ina ɗago kaina nayi an fincikoni haɗe goshinmu yayi, lokaci ɗaya na dafe kirjinshi ina runtsa idanuna.

Tare da rike rigarshi tam, ɗaukar hoton akayi a haka sannan ya tureni na faɗi kan kujera, haɗiye kukana nayi nasamu na bar gurinsu wajen yan uwana naje na fashe da kuka,

Duk suka ruɗe harsu Ahmad ɗin yana fitowa suka tsareshi da tambaya ɗaga musu hannu yayi dan sun cika mishi kunne yace.
"Ku tambayeta mana"

Yana faɗar haka yabar gidan muma gida aka dawo damu. Kallona,Rahimah tayi a nutse ina jan hancina tace.
Wai mike haɗaki da shine? Na lura duk zuwanshi sai yasaki kuka, kema sanin kanki iyayenmu bazasu taɓa zaɓa mana abinda zai cutar damu ba, amma mi yasa kike kuka ko baki sonshine tunda kika rahilah itama ba son Aman amma yanzun kiga yanda suka koma kamar zasu cinye kansu, kece baki lura ba, amma kiga yanda yake ɗawainiya da ita kamar zai maidata cikinshi, tsabar so ki kwantar da hankalinki don Allah kar iyayenmu su fahimci halin da kike ciki."

Dafata yayi idanuna na kara cikowa da kwalla nace.
"Rahimah wallahi tsoron shi nake ji, kuma duk zuwanshi sai ya min mugunta, ɗazun a can ɗin nan fisgoni yayi ya gwara min kaina da nashi, kinga gurin.".

Na nuna mata kwalla nasake cika idanuna.

"Wannan ba hujja bane, idan kika auna yanayinshi ba mai yawan kwaranniya bane haka Abban Chuchu ya faɗa min, suma suna son ganin yana walwala kamar kowa, amma haka ya tsarawa kanshi, ɗabi'arshi ce miskilanci ke ya dace ki shiga jikinshi ba shi zai shiga naki ba, ajiye wannan haukar zakiyi a gefe ki fara koyawa kanki rashin kunya, da wayewar dole, ki rage tsoro ki koyi tsiwa da wasu halin irinsu shagwaɓa, shirme kan ai nasan kece karshe a cikin gidanmu amma dole ki ajiye wannan sakarcin, ki zama jan wuya ki koyi iya kallon cikin idanunshi da rigimar dole yanda zaki canza mishi rayuwa amma ba ki xauna kina zare manyan idanu kamar mayya ba, idan yayi miki ki ɗauka ko ki ajiye a gurin. Ko gidanshi kika je matanshi suka ga baki da hikima da dabara zaki sha wahala dasu balle kuma shi namiji wanda ake kamashi ta hanyoyi da dama, ba yau Umma ta fara faɗar haka ba amma nayi mamakinki da kike zauna kina zubda kwlla akan namiji yana cusa miki bakin ciki tun awaje kenan kin nuna mishi baki da karfin kwatar kanki kenan hmm gwara ki ajiye tun wuri."

Tana gama faɗar haka ta juya min baya abinta, dan har ta gama ban daina kuka ba asalima kaman kara min kaimi akayi.

........Rike hannunshi tayi tana murmushi tace.
"My Man kaje AuntyNa tana jiranka karmu shiga hakkinta."

Lumshe idanunshi yayi cike da jin wani iri, janye hannunta yayi yakai kan Maranta da ya fara tasowa, ajiyar zuciya ya sauke kafin yace.
"Ina matukar son abinda ke kwance a nan da wacce take ɗauke dasu, Allah ya inganta min rayuwarsu nima nayi alfahari da nawa."

"Amin Ya Allah, ai da uwar da abin cikin duk nakane bana wani ba, kasan wani baya haihuwan ɗan wani, don Allah tashi kaje tana jiranka."
Dakyar da suɗɗin goshi ta tadashi yafita ɗakin, side ɗin Hindu ya nufa ko ina kace kace ba'a magana, haɗiye ɓacin ranshi yayi ya shige ɗakinta, a saman gado ya sameta tayi tagumi tana share kwalla,

Dakyar ya zaunaa bakin gadon yana kallonta cikin nutsuwa, bawai baya son hindu bane tsabar kazamtarta yasa yake kinta, janyota yayi jikinshi ganin haka yasa ta fashe da kuka bai wani damu ya dakatar da ita ba, saima zuba mata ido da yayi mikewa yayi ya ɗagata zuwa ɗakinshi,

Taimaka mata yayi tayi wanka ta gyara jiknta, sosai dan shi ya bi lungu da sako ya tayata cire gashin gurin da dattin sannan tayi wanka da taimakonshi, duk sai yaji yana jin ba daɗi dan tunda suka dawo taki barinsu a zauna lafiya, duk ranar girkinta a ɗakinshi yake kwana, taki ta nutsu ta gyara kuskurenta.

Koda suka fito ba laifi da yajata suka raya daren abin takaici ko jimawa ba'ayi ba ta fara mita ta gaji,

A take rahilah ta faɗo mishi a rai cike da bakin ciki ya sauka bao ida abinda yayi niyya ba.
.......

Tunda ya fita rahilah ta fashe da kuka, tare da rungume pillow haka take fama da matsanancin kishin Aman, dukda haka bata taɓa nuna mishi tana da zafin kishi ba, asalima da zaran ta ganshi take niman kishin ta rasa, kuka tayi mai isarta sannan ta mike ta shiga bayi tayi alola tazo ta fara sallah, ta jima tana kaiwa Allah kukanta da ya yaye mata kishin dake damunta.

Karshe a gurin ta kwana.

.......

Kwanaki sun gangaro har saura kwana biyu bikinmu, ranar laraba Rahilah tazo da katon akwatinta kowa yaganta yaga mai ciki dukda bai fito ba amma tayi wani jaaa, sai kwaɗayin azaba musaman Ayaba dan tazo mana dashi yafi cikin laida bai baki da fari, kuma irin manyan nan ba kanana ba,

Tunda ta warewasu Umma ta shige ɗaki da sauran ko kallon yaran Yayunmu da suke ce mata Auntyƴzamu ci. Batayi ba asalima gyara kwanciyarta tayi ta ɓare ɗaya tana kallonmu ta shiga lasar ayabar. Sam bamu fahimcin iskancin da take nufi ba sai da ta mike zaune tace.
"Kunga Yaren novel, duk ranar da kuka zama iskanka haka zakuyiwa mazajenku."

Zaro idanu mukayi da cewa.
"Kamar Ya???"

Dariya tayi sannan tace.
"Ku jakuna ba'ayin XxX ba tare da amotsa jiki ba dole kisan hanyar da zaki tadda mishi hankali, ko ce muku akayi kamar yanda bunsuru ke bin akuya haka ake abi....."

Allah bamu ji karshen maganarta ba, muka samfeee dan mun lura Rahilah ta lalace idanunta yayi mugun buɗewa, dama ya-ya lafiyar giwa..

*****
Gidan Mai nasara, a fakaice suka hura mishi wuta ta hanyar daina mu'amala dashi sai huda, sam bai wani damu ba dan ya bawa kowacce dama tayi haka,

Ana bikin saura kwana biyu ya shiga ɗakin Balkisu, ta zaune sanye da doguwar riga mai huda, shan y'ayan itace take, tunda ta amsa mishi sallama bata kuma ɗagowa ba, zama yayi kusada ita ya amshi bowl ɗin ya fara shan y'ayan itace hankalinshi kwance,

Sai da ya koshi sannan ya ajiye abin shiru ya ratsa tsakaninsu, riko hannunta yayi yana murza yatsun hannun tare da kallon fuskarta, ganin yanda take karɓan sakonshi yasashi fara wucce iyaka, bata wani damu ba ta mika mishi wuya suka kashe arna sosai, kallon fuskarta yayi a

hankali ya shafa gefen fuskar yace.
"Bansan ta inda zan fara faɗa miki ba, dukda na faɗa miki kwanaki zan kara aure kuma naga baki damu ba, shin mi yasa baki ɗabakka al'amurana a matsayin miji, baki tunanin wata ta shigo rayuwata ta sauya min ɗabi'a da halayata, karshe na karkata gareta zaki ji dadî haka ko? Bana fatan tauyeku amma kuna wasa da hakkina, akala wata biyu zuwa uku knn da wata ta bani hakkina sabida kowacce ku tana busy, kowacce ka taɓa tana da abinyi yaushe zan kira kaina da magidanci, amma ba damuwa duk yanda kukayi ɗaya ne."

Shiru tayi ta rasa bakin magana, sai ma narkewa da tayi a jikinshi tare da kara rungume shi, ɗago kai tayi cikin nutsuwa suka kurawq juna ido, ajiyar zuciya suka sauke kafin, ta janye idanunta tace..
"Duk matanka ban taɓa jin kishin kowacce su ba, sai wannan da zata shigo, dan tunkafin zuwanta muka ga sauyi daga gareka, abin da na lura kuwa nan gaba zamu iya rasaka ma, nidai don Allah dan soyayyar da nake maka karka juya min baya, ina sonka."

(Hmmm cinibibi inji yara humm daga baya knn.)

Sam bai wani ji farin ciki ba, sai ma mamaki da tabashi sun jima a gurin kafin ya mike ya shiga ban ɗakinta yayi wanka ya fito, bai tsaya ba sai ɗakinshi kwanciya yayi yanata juyi, can ya lalubo wayarshi gallary ya shiga ya fara duba hotunan da suka ɗauka na bikin da zai gabato,

Yana zuwa kan namu ya tsaya cak zooming yayi, sannan ya taɓe bakinshi sannan ya kashe wayar.

****

Ranar alhamis muka gabatar da taron lakca na mata, wanda yana cikin tsarin hidimar bikin wanda Manyan malamai na kungiyar da'awa suka gabatar a harabar makarantarmu, Ranar juma'a Yayunmu suka shirya kamu dan ban sani ba, sai da aka kawo min kayan nan na buga tsalle nace bazan saka kayanda rabin jikina a waje yake ba, karshe dai sai da aka ɗauko min alkyaba na ɗaura akan gown ɗin, haka suka gama shirmensu bansan mi sukayi ba,

Muna dawowa aka fara mana kunshi, tunda na kifa kaina nake kuka, har aka gama min ban ɗago ba dake jan lalle aka mana,

Gashinmu a gida aka gyara mana dan bamu cika saloon ba amma an gyara manashi sosai.

Ranar asabar da karfe tara aka gabatar da walima, sha ɗaya saura aka ɗaura aurenmu Maryam Sajida Omer tare Yunus Muh'd Marafa.
Sai Rahimah Hassana Omer,tare da Ahmad Zailani Bature,

Ɗaurin auren da ya haɗa mutane da dama, ciki da wajen kasa dan har da abokan

kasuwancinsu duk sun zo ɗaurin auren, baka iya gane hak'ik'anin gaskiyar abinda ke fuskar mai nasara sabida sanye yake da madubi,

Ana gama ɗaurin Aure aka ɗaukemu Zuwa ɗanki Malam murmushi yayi sannan yace.
"Toh mi zance musu bayan dai sunsan iyaka ta hakurin da na koya musu shi zance suyi bani da abinda yafi hakuri dan haka shi zance suyi tunda suka taso sun taɓa ganin wani abunda yafi hakurine a gidan nan dan haka suyi hakuri su zauna a ɗakin mazajensu lafiya."

Iya abinda yace knn aka fito damu,

Rahimah zuwa ɗakin Mama ni kuma zuwa ɗakin Umma, ina shiga na zuɓe a jikinta, kallon yayunmu tayi tace.
"Ku fita mana a ɗaki."

Fita sukayi ina kwance a jikinta shafa kaina tayi sannan ta ɗago min kai tace.
"Auta ina ganin ai nagama miki bayani tun a auren Rahilah kuma nasan zaki iya kome dan kare martaban gidan nan, auta wata rayuwa tana can tana jiranki gwargwadon hakurinki gwargwadon kimarki a ido mijinki, auta bani da haufi akanki amma ina da shakku aksn ɗabi'arki ta tsoron bak'in fuska, ki jajjirce ki zama jaruma kema aure ya kaiki ba tsoron wata ba, bance ki rena su ba, amma ban yarda wata ta nuna miki yatsa ki zauna kinakuka ba, koda wasa karki nunawa Kishiyoyinki bakya shiri da mijinki da zaran kika nuna musu baki shiri dashi da wannan abin zasu yake ki har kibar rayuwarsu, Auta so nake kizama fitar numfashin Yunus ki xama bugun zuciyarshi, so nake ki zama nutsuwarshi, ki zame mushi haske rayuwarshi autana ina son ki zama bango yayinda yunus ya ɗibo gajiyarshi ya jingina a gareki ina tsorataki da lalaci, ragonta, rashin iya magana, rashin ɗa'a, ban baki shawaran rabashi da kowa nashi ba, Maryam ki zama adila karki saka ido akan abin hannunshi idan yabaki ki nuna mishi godiyarki, sannan kice ya kara yawa Iyayenshi hidima, Auta bari na baki wani sirri karki taɓa yin sati baki nime wani abu kin bashi ya kaiwa Iyayenshu musaman Mahaifanshi da matar babanshi, auta kannen shi da sauran danginshi ki kyautata musu nina faɗa miki wannan da kanki zakice Umma abinda kika sani ga tukwaicinsa, ki daidaita rayuwarku sannan idan ya karkata ki dawo dashi kan hanya, Kiyi imani da Allah zai baki mafita da nasara akan komi Maryam Sajida ga wannan alkur'ani ne sai hisnul musulim, sune iya abinda zan baki, ni bana boka bana malam amma nayi imani da Allah Maryam Sajida ban umarceki da shan maganin mata ba, dan bai gyara komi sai ɓata aure kiyi tattalin kanki da lafiyarki musaman alauranki baya bukatar wani abu bayan ruwan zafi, Maryam! Maryam! Maryam! Sau uku nakiraki ki nutsu dan akwai lokacin da bazan iya taimakonki ba, juriyarki da hakurinki sun isa su karɓeki, karki taɓa bijire mishi, matukar kinsan ba hakkin wata ya tsalaka ya kawo miki ba, ni dai na umarceki da ki zauna lafiya da kowa, banda saurin fushi da fusata Allah yayi miki albarka, yasa nan da wasu watanin an kawo minke ce dan sunan wanka Autana tayi girma ta zama mace koda yake da sauranki dan bakisan Waye zaki zauna dashi ba, aikin gabanki ki sannan waye Yunus."

Kuka nake tare da kamkame Ummata ina cewa.
"Umma don Allah karku kaini na fasa zuwa ina son zama daku."..

Shafa kaina tayi sannan tace.
"Hakuri zakiyi dan zaria za'a wucce dake, kuma ana jiranku Auta keda zaki zauna a garin nan miye na kuka kuma, idan kika samu kulawar mijinki mantawa zakiyi da Ummanki, maza tashi ana jiranki karki ɓata musu lokaci kinji autana."

Kiransu Shema'u tayi suka fitar dani, sannan aka kawo mata Rahimah kamar yanda tayi min haka ta mata, ashe mama amarya kan babu abinda ta iya cewa, sai Allah ya baku zaman lafiya kinga halin da nake ciki ki zauna lafiya da mijinki nima shine nawa kwanciyar hankalin tashi kuje ana jiranku."

Aunty Asma'u da Aunty Hamdiya da gausiya suka tawo min, Aunty Shema'u da Aunty Shukrah da Matar Ya hayat, suka raka Rahimah, katsina.

Rahilah kan bata bisu ba zaria ta biyo mu, dakyar aka rabani da jikin Umma aka sakani a mota........

*Ina taya dukkanin musulmin faɗin duniya murnan Sallah babba, Allah yasa'ayi lafiya ya bamu lafiya da zaman lafiya......Barka da Juma'a ayi shagalin sallah lafiya ina jiran ɗaukanina 👌😹*

#HWA.......
#MATARSO........
#Mai_Dambu.......
#Danban nake da sauran.......
[8/25, 2:59 PM] Real Mai Dambu: 🌹🌹🍀
*MATAR SO*
🌷🌷🌻

*MAI_DAMBU*
*Wattpad:Mai_Dambu.*
*HAZAKA WRITER'S ASSO*
(HWA)

Da sunan Allah Mai Rahama Mai Jinkai....

Dedicater To Hafsat Abubakar💋

_Wannan buk ɗin hakk'in masu shine idan kinsan baki saya ba karki karanta, mai fitarwa kuma ki duba girman Alkawarin da kika ɗauka na cewa bazaki fitar ba, tunda nace idan kinsan zaki saya ki fitar na Yafe ba sai kin saya ba_

*BOOK 1👈*

*Page.....15*

Mu Yan zaria tafiyar mintuna arba'in da biyar ya kaimu can,

Nan naga tarɓa na musaman yan uwan Mai nasara, da danginshi, wani irin hidimar biki suke kaman akan wannan auren aka fara biki a gidan.

Dan shagali suke sosai, a ɓangaren ango bai iso garin zaria ba sai karfe shida shima dan ance mishi, Hajiyarsu tace kar ya kuskura yaki zuwa Liyaffan da aka shiryane, shine ya ɗibo jiki tare da Yarshi suka tawo.

Koda ya shiga gidan dakyar ya aro murmushi ya ɗaura akan fuskarshi, idan kai mishi magana sai dai ya wangale maka jerarrun fararen hakoranshi, tunda ya shiga gurinta suka gaisa da ita da sauran Yan uwanta, ya fita zuwa gurin Mama kilishi suka gaisa muna cikin ɗaya ɗakinta, muka tsinkayo muryanshi, cikin sauri Rahilah tafito suka gaisa tace mishi.
"Don Allah ka nimo min Ya Aman kace ya amanta dani ne, har yanzun bai kawo min aikar ba."

Jinjina mata kai yayi ya fita, tsaki yayi a ranshi yace.
*Ai ga illar auren yaran yarinya karama tasaka kato a gaba da fitina, ayi kaza a bar kaxa, tsabar rashin kunya ko mi mutum zai samu a jikinsu,duk ranar da wanca Yar tayi ta kawo min reni zaneta zanyi abuna.*

Yana fita kuwa sai ga Aman rike da katon leda yana niman wanda zai aika cikin gidan Hararanshi mai nasara yayi yace.
"D'an iska ka haɗa gurbi da jinjira, ta rena kowa gani take kaman kaine kaje wai tana jiran sakon da tabaka."

Murmushi Aman yayi cikin jin daɗi yace.
"Nifa ban rena mace ba. Sabida nasan amfaninta ainun, sannan kai da kake tunanin dan mu haɗa gurbi da ita hmmm, ina tausaya maka mai nasara dama can ina son Rahilah kuma akayi dace tafiyarmu ɗaya, ina samun abinda ban samu ba a tsawon shekarun aurena da hindu sai na renata, ina tausayawa ranar da zaka faɗa hannun Maryam Sajida idan duniya gatarka ce sai ka rena gatan da suke maka, kuma kaga jinjirata cikina ne a zaune a womb ɗinta karshe knn, ta ɗauke ni ta ɗauki gudan jinina."

A kiɗime Mai Nasara ya ɗago idanunshi a waje yace.
"Ciki!!!"

"Kwarai da gaske, wannan shine na biyu a paris tayi ɓarin sati ɗaya zuwa biyu, kaga da Allah yasoni da rahama shine ya kara min wani. Shawara kyauta ka dage ka shawo kan Jinjirar ka, in

yaso ana mika maka ita ka buga.."

"Kaii bana son iskanci, tayita zamanta mana ji min banza namamajo kawai." Yanda mai nasara ke faɗa zaka ɗauka wani saɓo akace ya aikata, sororo Aman yayi yana kallonshi, can sai Huda tafito mika mata aikan Rahilah yayi takai mata.

****

Muna zaune sai ga huda da sakon rahilah nan muka baje kolin ciye ciye, tana gama ci yaki zama dole sai da tayi amaye shi tasss, sannan ta dawo ta kwanta sake kiranshi tayi tare da fashewa da kuka tace.
"Ya Aman abinda naci yaki zama nayi amanshi ka nimo min Ayaba gashashe, zanci."

"Ok Baby bari yanzun zan kawo miki kinji."

....... Kallon Banza Mai nasara yayi mishi cike da jin haushi yace.
"Amma kayi girman banza ynz fita zakayi ka nimo mata wani abinci."

"Kasan Allah Yunus zanci Ubanka, wallahi zan zabga maka rashin mutunci, yarinyar da laluran ciwo bai hanata ɗaukar hidimata ba shine zan wulakantata? Kasan hakkin mace kuwa akan mijinta, toh bari kaji hatta kishiyarta Rahilah tana kokarin sauke hakkinta balle ni, Idan har mace zata iya sadaukar da lafiyarta da rayuwarta gurin ɗaukar cikinka, kuma ta iya baka kanta dan sauke hakkinka dake kanta toh babu amfani tasami ciki daga gareta baka tausassa mata ba, sabida ai laluran ba zuwa tayi dashi ba, a gurinka ta ɗauka, Toh mi yasa ma nake ɓata bakina bayan duk matanka babu wacce ka taɓa mata soyayyar gaskiya duk katarasu ne dan suna sonka bawai kana sonsu ba, idan kayi dace da macen da kake so komi tayi bazaka kyamaceta ba dakanka zaka kai kanka inda baka zata ba banza wawa kawai."

Yana gama faɗar haka ya kirata a waya yace.
"Kifito ina jiranki."

Ba musu tafito, dakyar tun kafin ta iso yaje ya rungumota, har mota ya kaita daga nan suka bar gidan, inda suka shiga yawon niman masu saida gashashen Ayaba dakyar suka samu, daga nan wani hotel ya kaita.

Wanka ya taimaka mata tayi inda suka lalace a gurin, koda suka fito bai ɓata lokaci ba, gurin ya lula da ita duniyar ma'aurata dan yasan inba haka yayi ba komi taci zata fitar suna gamawa wanka suka koma sannan ya zauna taga taci ta koshi har da gyatsa shafa bayanta yayita yi har wani barci mai nauti yayi gaba da ita, zare towel ɗin yayi yana kallon kirjinta da suka cika sosai gado ya mai da ita sannan ya zare towel ɗin ya shagala a kallon halittar matar shi. Wani sabon fitinar son kasancewa da itane ya bijiro mishi, a hankali yake binta har ta farka rike shi tayi gam har ya ɗago murmushi tayi masa cikin muryan barci tace.
"Baka gaji bane."
Girgiza mata kai yayi da birkitattun idanunshi yace.

"Ban gaji ba Raaka ina bukatar more."

Rufe mishi bakinsa tayi daga nan kuma ta ware akabawa Juna hakkin love.

.........Tunda Aman ya tafi yabarshi da tunanin abinda ya faɗa mishi, a hankali yayi tsaki yafi sau goma kafin ya mike yabar gurin....

*****

Yan katsina basu isa katsina ba sai biyar na Yamma, inda suka samu ana walima a gurguje aka shirya Rahimah aka fito da ita tayi kyau kuwa,.

Karfe shida aka tashi, dawo da ita bangaresu akayi, takwas daidai aka sake fita wank dinner wanda Yan uwanshi suka shirya a wani hotel, toh da aka kawo mata kayanta aka gama shiryarta cikin doguwar gown fari mai ratsin pink da milk haka ma takalmin, a nutse tafito har inda motarshi yake buɗe mata akayi ta shiga, daga nan aka rufe kanta a sunkuye tace.

"Ina wuni."

"Lafiya Princess, ya gajiya da jama'a."

"Alhamdulillah"

Shiru ne ya ratsasu kallonta yayi yanda ta takure kanta,murmushi gefen bani yayi a ranshi yace. *Da alamu yau zan baje, amarcina.*

Har gurin dinner suka isa, daga nan aka fara hidima har aka tashi karban key motar yayi a hannun Faisal yajaso sai gidanshi sake cikin gari, jikinshi na rawa yayi parking a cikin gidan bayan an buɗe mishi gidan. Dake dare sosai, babu wani hayaniya ya fito da ita yayi suka shiga gidan.

Duk jikinta ya mutu, suna shiga falon ya sunkuceta yayi cikin bedroom da ita nan ya taimaka mata ta cire kaya, tana zuwa kan bra ta juya mishi baya ɓalle bra ɗin yayi, kamkame jikinta tayi, zuwa yayi ya rungumeta ta baya hannunshi nakan waist ɗinta zame under ɗinta yayi anan jikinta ya sake ɗaukar kerrrma kamar wacce aka watsawa ruwan sanyi.

Yana kai komi kasa ya juyota tare da kallon cikin idanunta amma ta rufesu gam kwalla na sauka daga samansu, bai ɓata lokaci ba ya kashe wutar ɗakin ya dawo kusa da ita, yana zuwa yayi ɗauketa cak sai saman gadon.

Abinda Ahamad yake kauna kirjin mace toh gasu nan yasamu, kamar zai haukace haka yake binsu sosai, dalilin da yasahi ɗaukota kenan. Amna ganin ya gansu sai yaji yana muradin raba manhaja da ita, sosai ya murza kirjin yanda ranshi keso ba tare da wani fargaba ba, ya tun kari fadar karshe da zai kaishi duniyarta sai mi jin yayi Yaren novel ɗinshi ta koma kamar zakaran da yasha dukar ruwan sama,

Sake gwadawa yayi yaga still haka ne, a tsorace ya ɗago yaga yanda ta rufe fuskarta tana kuka kasakasa, sake kokari yayi ta koma daga haka bata kuma ko matsawa ba, a gigice ya

faɗa ban ɗaki yana shiga tana mikewa kamar itaba da sauri ya dawo yayi kanta koda ya tunkari Rahimah ji yayi sandar girmar tayi lakaf.
Jikinshine yayi sanyi ya janyota tare da rungumeta yana sake ajiyar zuciya cike da bakin ciki mike shirin faru da shi.

.......
A ɓangarenmu anyi liyaffa lafiya tunda muka dawo, Washi gari da safe aka fara gudanar da buɗan kai wanda ya haɗa cincinrindon yan uwa da abokan arziki, banga Rahilah ba ashe sun wucce katsina tun safe.

.......

A katsina, niman Rahimah aka shiga yi, can Faisal yake faɗa musu ai suna tare da Ahmad, shiru Ummi tayi ta shiga gurinsu Aunty Shema ta basu hakuri.. Basu wani damu ba akan haka dan burgesu tsarin Ahmad yayi.

..... Da asuba ta rigashi farkawa a hankali ta xare jikinta zuwa ban ɗaki tayi wanka ta maida kayanta, ta fito kanta a sunkuye ta sameshi a zaune raɓewa gefe tayi ta tsaya, ɗago kanshi yayi tare da mika mata hannunshi a hankali ta isa gareshi zaunar da ita kan cinyarshi yana kallon yanda ta sunkuyar dakanta tana wasa da farcen hannunta da yake jurwaye da lalle ja da baki. D'ago kanta yayi yana jinjina girman matsalarshi aynx da take kan cinyarshi yana jin yanda abin tayi sanyi, wanda kuma ba haka bane dan tunda ta janye jikinta yajishi lafiya lau, tsoro da al'ajabi suka mishi diran mikiya.

"Kiyi hakuri na kawoki guri na dameki ko? Yanzun zan kaiki gida." Ya faɗa mata.

Maida ita gado yayi, ya shige ban ɗaki dafe goshinsa yayi jin yanda abin ta mike, tare da kulewar maranshi.

A daddafe yayi alola da wanka, yafito sallah yayi dan ya lura babu abinda zata rufa tayi sallah, yana idarwa ko addu'a baiyi ba, ya mike tare da cewa.
"Preety muje gida kiyi sallah."
Gyaɗa mishi kai tayi tare da mikewa suka bar ɗakin bayan ta rufa da mayafin gown ɗinta.

...... Cikin Yan mintuna suka isa gidan, a falo suka sami Ummi yana shiga dake shine a gaba harara ta banka mishi tace.
"Allah Ahmad kafita idanuna, bana son ranshi hakuri, ina ka kaimusu yar mutane."
Matsawa yayi ya riko hannuj Rahimah ya isa gaban Mommy ya danka mata ita, ko magana ya gaza ya juya a binshi, jikinshi a sake tsabar tashin hankali.

Mikewa Mommy tayi takai Rahimah ɗakin da su Aunty shema suke, da sallama ta shiga suka gaisa cike da kunya tace.
"Gata nan ya dawo da ita ku bata duk wani kulawar da ta dace, bari na nima mata abinda

zataci."

"Toh mun gode." suka ce mata, dake sun iya taya ɓera ɓarna take suka shiga haɗa mata ruwan zafi da yanda zata gasa jikinta duk kunya ya buwayeta, a haka tayi ta sake alola, dan babu karya kirjinta na zafi amma da tayi wanka taji daɗi sosai, tana fitowa tayi salla, tana idarwa tabi lafiyar gado dakyar taci abinci nan kowa ya damu ita kuma gajiyar matseta da yayine yasata barci dan bata samu barci ba.....

Bata tashi ba sai sha biyu nan ta mike tashiga bayi tayo alola tazo tayi sallah, sai a lokacin suka lura da babu wani sauyi na anyi wani abu da ita, nan suka shiga tambayarta ana haka Rahilah ta shigo take, ta zauna aka cigaba ta titsiye Rahimah banza tayi musu ta koma gado tayi kwanciyarta, mi Rahilag zatayi banda dariya har da cewa.
"Hooo My Hassana an shiga kwaryan Manyan anyi Ayabar maza, faɗa min ya tafiyarki bata sauya ba."

Duka Rahimah takai mata, sannan tayi kasa da murya tace.
"Banza babu abinda yayi min, kawai kirjina ke min zafi, musaman kan boons ɗina."

"Hmmm Pratical aka fara, ki jira sauran aikin yana gaba."

Lumshe idanu Rahimah tayi sannan tace.
"Hussainata haka Yaren novel yake."

Wani shegen dariya Rahilah tasaka wanda yajanyo hankalin Yayunsu da Yan uwan Mama Amarya.

Ganin an tsaresu da idanu yasa suka shige bargo Rahilah tace.
"Maybe garin ya raya sunnah dake kika tsorata kika ki ba."
Girgiza kai tayi tace..........

Barka da Sallah....Kuyi maneji kusan shagalin sallah ake, kuma ina son Bawa, *My Hero* lokacina dan kar na shiga hakkinshi na shiga naku.......shi yasa na saci jiki nayi muku typing......

[8/25, 2:59 PM] Real Mai Dambu: 🌹🌹🍀
*MATAR SO*
🌷🌷🌻

*MAI_DAMBU*
*Wattpad:Mai_Dambu.*
*HAZAKA WRITER'S ASSO*
(HWA)

Da sunan Allah Mai Rahama Mai Jinkai....

Sadaukarwa Ga Yan grp ɗin Matar So....
Dedicater To Hafsat Abubakar💋

_Wannan buk ɗin hakk'in masu shine idan kinsan baki saya ba karki karanta, mai fitarwa kuma ki duba girman Alkawarin da kika ɗauka na cewa bazaki fitar ba, tunda nace idan kinsan zaki saya ki fitar na Yafe ba sai kin saya ba_

*BOOK 1👈*

*Page 16*
"Kaiiii ba haka bane My half kawai naga da zaran yayi niyyar, toh bansan yanda zan miki bayani ba but akwai yar matsala wacce bata wani girma ba,"

Shiru tayi tare da barin zance dan bata ga wani amfanin hiranta sirrinsu ba.
.......
Har akayi buɗar kai Ahmad yana nan sakaka babu laka a jikinshi,
Har washi gari da aka kamo hanyar dawowa gida dan yanzun yake jin abin sosai gabaki ɗaya y'ay'an halittarsa ta motse, kuma yaja bakinshi gum.

........
Muma da azahar muka bar garin zaria, muka dawo gida tare da huda, wacce ta makale min a unguwarsu Rahilah gidan yake kusa da juna muke, sosai.

An gama kintsa min gidan shida saura sannan kowa ya watse bayan sun min dogon nasiha bin miji.
Nayi kuka sosai bayan tafiyarsu, daga ni sai huda haka muka zauna har bayan isha, wajen tara muna zaune a ɗakina ya buga kofar huda ce ta mike taje ta buɗe kofar mika mata laida yayi yace.
"Princess zaki xauna ne ko zaki gida."
"A'a daddy zan tafi idan kace na tafi."

"Nop jeki yi zamanki, mu kwana lafiya." ya juya da babban rigarshi.

.......
Rahimah itama suna gama mata abinda zasuyi suka ɗauketa zuwa gurin Hafsa a mutunce suka gaisa kafin suka ce.
"Ga Kanwa nan mun kawo miki da fatan zaku zauna da juna cikin amana da amincin."

Dariyar renin hankali tayi musu kafin tace.
"Ai ynz ba'a karɓan amanar kishiya zama tazoyi idan zata iya zama ga fili ga me doki Allah ya bada sa'a kowa tasa tafisheshi."

Tana gama faɗar haka ta mike tare da barinsu a falon.
Shiru sukayi kafin aka fita da rahimah nan aka mata nasiha,

Kafin suka watse kowa yana nazarin furucin Hafsa...

Aman da Ahmad suka shigo gidan, kallon Aman yayi cike da son faɗa mishi matsalar shi amma abin mamaki ji yayi harshensa yayi nauyi dan dole ya haɗiye maganar har ciki aman ya kaishi sannan yayi mishi saida safe, dan tunda suka iso yakai Rahilah gida tana kukan ciwon jiki.
Yana isa gida ya sami hindu tsaye taci uban ɗamara zatayi dambe da Rahilah sai zaginta take, ganin motarshi ta sake buɗe sabo masifar. Fitowa yayi ya kalleta sam baya son damuwa, yana isa gurinta ya riko hannunta suka shiga ciki yace.
"Ke ba abin kunya bane, ace kina ihu da kishiyarki ai saita renaki."
Buge hannunshi tayi cike da masifa tace.
"Ai dole ta renani, tunda ka iya buɗe kafafunta ka shigeta ba dole taga kanta daidai dani ba, mi zan nuna mata wanda bata sani ba."

"Amma dai kanwarki ce tunda kinfita hankali da sanin ya kamata yarinya ce... "

"Kutt Mandara ni kake faɗawa matarka yarinya ce, idan da kasan yarinya ce wallahi bazaka taɓa shigarta ba, nice zaka rena min hankali kace yarinya ce sabida ga jaka kasami karamar karuw..."

"Ya isa haka bana son kazamar kalmominki nan, eh naji nasami yarinya zan rena miki hankali Hindu dubeki fa, daga sama har kasa zo muje kiga yanda ake rayuwar aure."

Fincikar hanunta yayi har falon Rahilah da take kwance barci yayi gaba da ita, falon sai kamshi yake tsabar yaji turaren wuta da room fresh, ita kanta Rahilah wasu shegun sexywear ne a jikinta, ta kwanta dasu gashi taci wani mugun kwalliya, dukda ba girkinta bane amma zaka fahimci tayisu ne dan faranta ran mijinta kallon Hindu yayi wacce ta mutu da mamakin yanda Rahilah ta koma, taɓe baki tayi ta juya abinta tabar musu falon, tare da cin alwashin sai ta wargaxa soyayyar da tagani a tsakaninsu.

Bayan fitarta ya isa gaban Rahilah ya ɗauketa cak har ɗakinta addu'a yayi mata, sannan yasaka hannunshi ya ɓalle bra ɗinta ya ajiye yafita, duk tana jinshi matukar ta motsa toh sai san yanda tajashi suka shiga hakkin hindu ita kuma bata burin haka.

.......
Bayan tafiyar Aman, ko leka ɗakin Rahimah Ahmad bayi ba, kwanciya yayi a ɗaya ɗakin, abin duniya ya dameshi, tun Rahimah nasa ran zuwarshi har tayi barci.

****
Washi gari da wuri muka tashi, tun bayan sallar asuba na fara karatu har gari yayi haske, abinci

aka kawo mana daga gidan Rahilah, mai kyau da daɗi.

Bayan munyi wanka muka ci nida Huda, muna zaune najiyo muryanshi, kafin kace mi har na kware mikewa nayi a guje nayi sider ɗina ina tari.

Dama kunune, kuma ba komi ya janyo haka ba tsabar tsoronshi da nake jine. Shafa kan Yarshi yayi tare da bina da ido taɓe baki yayi yace.

"Queen nafita."

Gyaɗa mishi kai tayi, yana fita tana shigowa daga jikin kofar ta kalleni hannunta harɗe da kirjinta tace.

"Ban fahimce ba, kima nufi haka kema zaki bi layin sauran Matanshi Aunty Mom, ina murna Daddyna ya auro wayayya ashe mafarki nake, daga jin muryanshi har da kwarewa. A gaskiya bazan ɓoye miki ba Mahaifiya mace yake nima da zata gyara mishi rayuwa frm today dole ki fara hidimar gidanki, Aunty Maryam nasan kin girmeni amma ni nasan abinda daddy ɗina yake so mutum ne mi bukatar kulawa, so yake a kambamashi kamar wani sarki, so yake a nunawa duniya shi mutum ne, amna duk da haka yana da matukar adalci dan mutum ne mai ra'ayin rik'au, inso samune yana bukatar abincinmu na hausa, yana bukatar abubuwa wanda ni kaina bansan iya adadinsu ba, yau zan koma sabida gobe ina da exam zan tafi makarantar kwana, Aunty mom bana son na dawo nasamu baki kwace daddyna a hannun sauran matanshi ba, kaiii har da Mahaifiyata better ki daina tsoronshi dan ba amfanar dake ziyi ba."

Tana gama faɗar haka ta juya tabar min ɗakin jikina yayi mugun sanyi da abubuwan da tace, kuma gaskiya ne amma bazan iya ba.

.......

"Yar Malamai ya Amarci da fatan anyi kwanar amarci ko? Hey Ahmad naga Kwailarka kirjinta a cike yake kasamu yanda kakeso kuwa, dan nasan Yaran malamai akwai kamun kai, koda yake nasan virgin ce ma, amma ya kaiii matsayi toys ɗinka tayi aiki kuwa yanda ya dace, yanda naga kake rawan kan nan."

Kurrrr yayi mata da ido cikin nazarta abinda take faɗa musu idan ya fahimta tana da masaniya kenan da lalurashi, murmushi yayi ya mike rungumar ta yayi yana dariya yace.

"A duniya akwai mace da xata iya da kayan aikina ne sama da Amaryata, tambayeta"

Juyawa yayi ya tsare Rahimah da take jin kamar ta fashe da kuka, yace.

"Sugar faɗa mata yanda kikayi sucking penis ɗina, ki faɗa mata yanda nayita moving da slowing a vaginal ɗinki, Hooo Baby faɗa mata."

Murmushi karfin hali tare da mikewa ta iso gabanshi kaii hannunta tayi kirjinshi tana dariya tace.

"Hmm ai faɗar irin abinda naji jiya a tare da kaii ɓata lokacinw nidai nasan koma Ya-ya ne naji daɗin da kowacce mace take ji, ai ka manta ranar Dinner da kayita squeezing boons ɗina ko ba haka ba, nasan kana sonsu kuma ko yaushe kashirya Am ready."

Fuuuuu tayi waje, ranta a ɓace, ganin haka rahimah itama ta nime barin falon, janyota yayi ya

rungumeta ta baya cikin sanyi murya yace.
"Karki sake barin kishiya ta nime rena miki hankali,naji daɗin haka amma bance a rena min matata ba."

Duk abinda yake faɗa hannunshi nakan na fulaninta, cike da jin daɗi amma tuna halin yake ciki yasashi saketa, yana zargin hafsa da sauri yabar falon,

Can kuryan ɗakinta ta shige tana kuka tace.
"Ammy wallahi karya matar nan tayi miki, babu abinda mukulinta yake dan tun a katsina ya kusanci matarshi taci kuɗina abanza Allah ya isa min kona abin banza zanyi na shiga cin uban Yarinyar."

Komawa yayi ya dawo falo murmushi yayi ya zauna can jin motsinta ya sashi mikewa ya shige ɗakinshi yana kallonta, tafito da ashana da mukulin zata kona, fitowa yayi yace.
"Bani.."

Ya mika mata hannu, ganin babu wasa a fuskarshi yasata mika mishi cikin sanyi murya yace.
"Bani da hakkinki shi yasa kika faɗa abinda kika kula, idan nasakeki yanzun cewa za'ayi dan nayi sabon aure amma ki zauna zan duba al'amarinki."

Yana gama faɗar haka yabar gidan baki ɗaya, gidansu Aman ya nufa da maganar gurin Mamie ita ya iya bawa yayi mata bayani a takaice.

"Kaje gida zan kira Yayana nayi masa bayani, kuyita addu'a Allah ya azurtaku da shu'uman matane sai du'a'i."
Godiya yayi mata yabar gidan, jikinshi yayi matukar sanyi.

........Koda mai nasara ya isa gidanshi Fareeda da Aneesa ya samu a falo sunci uban kwalliya, da sallama ya shiga dakyar Aneesah ta amsa, fareedah kan tsaki tayi abinta.

Kaii tsaye ya wucce ɗakinshi, yana shiga yaga ko ina duk kura tsaki yayi ya ɗauki abinda zai ɗauka yabar gidan. Suna ganin yafito suma suka ɗauki mota tare da Mufida sai Gra.

Ina ɗakinshi na gama wanke bandaki na gyara gadon tare da haɗa burne nasaka turaren wuta, yana gama turara ɗakin nayi fitowata.

Falon tattara takardun da ya watsar nayi, na zuba akan wani stool dake falon sannan na share falon na goge kuran, tana gamawa tafito sanye take da riga da skirt na blue lace, ta kima uban ɗaurin ɗan kwali rike da tsintsiya take, ta nufi kitchen, tana ajiye kayan hannunta ana dukar kofar shigowa falon da garammm.

Da sauri suka fito Fareeda da Aneesah tare da Mufida, sun tsaya cirko cirko, tsaki huda

tayi ta koma kitchen tana yankq albasar da zasu ɗaura abincin rana.
Zaga gidan Aneesah take cike da bakin kishi tana kallon ko ina, tace.
"Lallai kuwa, muna tare dashi yasayi filin ya fara ginawa shine zai bimu da sakayyar mana kishiya ya kawota ciki toh wallahi za'a lalata kowa ya rasa."

"Hmm bari namiji ba amana wato ga bayinshi ya ajiyemu a gida kamar akulki shine ya kawo Yar malamai katon mansion ɗin zata kuwa ci Ubanta."

...... Har gabana Mufida ta tako tana kallona cike da tsana tace.
"Ashawo kawai, i hater you foolish nonsense kuma abinda kika bawa Daddynmu ya juya mana baya sai kinyi dana sani, bitch kawai, kalleki kamar mi gaskiya kwaɗayi da son abin duniya yasa parent ɗinki aura dake da wur....."
Tauuuu na ɗauke yar banza da mari, wanda yayi daidai da shigowarshi. Cak ya tsaya yana kallona tureta nayi, zata faɗi ya tareta yana min wani mugun kallo cikin kirsa da kisisina Fareeda tace.
"Ikon Allah daga yarinya tace, tana sonki zaki hauta da bugu sai kace kin sami jaka, dan kin sami kan Ubanta sai ki lahanta mishi y'a gwara da kagani dai."

Kuka Mufida ta sake tare da rike gurinda na mareta, tace.
"Daddy kawai nace tayi maka magana mudawo gidan nan ne shine kawai tace min ni ɗin banza ni ɗin wofi ta tsanemu har da Mommy, kuma idan muka dawo gidan nan sai tayi poising ɗinmu, ita ta haifa maka yara, tunda baka sonmu shi yasa ka ajiyemu a can ita kuma ka akawota nan..."

"Ya isa Baby hold it."

Ta kowa gabana yayi ranshi a bace ya kifa min mari, sai da na zuɓe a kasa cikin zafin rai, yace.
"Uban waye yace miki ina sonki ina son haɗa gurbi dake kinsan yanda nake girmama Yarana da zaki ɗaga hannu ki mareta banza irinki ne zan kira mace baki ga matana bane karamar munafuka."
Sake ɗaga hannu yayi zai mare ni huda tace.
"Daddyyyyyyyyyyy! Mi tayi maka da zaka bugeta daga zuwanta jiya jiya."

"Toh mother teresa dukana tayi kuma tace zata kashe ni, har tureni tayi fa aiga Daddy nan."

"Karya ne, da zata dake ki dani zata fara duka wannan wani irin bahaguwar Rayuwata, Wallahi sai na faɗawa Hajiyarka yau ba gobe ba, ku kuma munafukai azzalumai yana kanku wata rana, Am sorry mufida zaki girbi abinda kike aikatawa, for first time Daddy Am really hater you, bana sonka sabida kai ba adali bane, kamar yanda kake cewa baka sonta itama bat...."

"Ya isa huda babu kyau, mahaifinkine kuma yana da ikon zarta dakowani hukunci akaina, nifa matarsa ce bana son kina shiga rigimarmu, yawan faɗarmu yawan fahimtar juna, karki sake

ɗagawa mahaifinki murya indai nice na yafe mishi ko a gaban Ubangiji bana fatar ya kamashi da hakkina, ita mufidah kuma Allah ya shiryeta, Mijina haske rayuwata akwai abinda kake bukatane bayan haka a shirye nake na amshi hukuncika fiye da haka ma"

"Aunty Mom!!!"  Huda ta kira sunana cikin kuka ganin yanda na zuba gwiwana a gabanshi ina share kwallar dake bin fuskana......

😂😂😂😂😂😂 *So min taɓi ango ya dafa Amarya kuyi hkr mu kare satin sallah a 3 readmore karku manta da hidimar sallah ake afuwa....*

[8/25, 3 PM] Real Mai Dambu: 🌹🌹🍀

*MATAR SO*

🌷🌷🌻

*MAI_DAMBU*
*Wattpad:Mai_Dambu.*
*HAZAKA WRITER'S ASSO*
(HWA)

Da sunan Allah Mai Rahama Mai Jinkai....

Sadaukarwa Ga Yan grp ɗin Matar So....
Dedicater To Hafsat Abubakar💋

_Wannan buk ɗin hakk'in masu shine idan kinsan baki saya ba karki karanta, mai fitarwa kuma ki duba girman Alkawarin da kika ɗauka na cewa bazaki fitar ba, tunda nace idan kinsan zaki saya ki fitar na Yafe ba sai kin saya ba_

*BOOK 1👈*

Page....17

Tsaki yaja min tare da juyawa ya zabgawa Matanshi harara, na mi ya kawoku juyawa suka a birkice sabida ranshi na kara ɓaci. Wuccewa yayi ya shige ɗakinshi zama yayi a bakin gado tare da dafe goshinsa, kanshi na kara zafi.

...... A hankali Huda zo inda nake ta rungumeni, kuka ne ya kwace min wanda bansan iyarkashi ba.

Dakyar na mike na haura ɗakina dake sama akan kujera na zube na cigaba da kuka.

Kiran sallah azhar ya ɗaga ni nashiga bandaki, alola nayi fuskana na kalla a madubin ban ɗakin naga fuskana sun kumbura, musaman inda ya mare har hannunshi sun kwanta Girgiza kai nayi na fito na shimfiɗa abin sallah na fara, ina idarwa Huda na shigowa ta shirya tsaf cikin sanyi murya tace.

"Aunty Mom zan tafi, gidan aikine a gabanki kici ko ta cinyeki ba lallai bane na dawo amma kafin tafiyata zan zo."

Tana gama faɗar haka ta fita da sauri, bin bayanta nayi sai na dawo na buɗe jakana na ciro kuɗi wanda nasamu a buɗan kai na sauko da gudu, tsabar karsu tafi ban bata wani abu ba,  duk hankali na yatafi da ita dan naji dirin motarshi.

Gummm naji bayan nasauko daga step, garin gyara rikon kuɗin naji nayi karo da abu baya nayi zan faɗi duk kuɗin suka watse, a kasa saura kiris na faɗi da baya sai ji nayi an rike k'uguna tare da tallafeni, a firgice na ɗago ina kallonshi nayi a tsorace.

Tunkuɗe ni yayi tare da buga tsak'i, tare da barina a gurin ajiyar zuciya na sauke tare da tattara kuɗin na sake fita a falon.

Har gurin motar na isa na kwankwasa glass ta buɗe tana murmushi nima mai da mata murmushin nayi sannan zuba mata, kuɗin cikin motar nace.
"Don Allah kafin tafiyarki, ki zo mana."

Ƙallon uban tayi sannan ta juye gareni tace.
"Aunty Mom nagode amma.."

"Kuna ɓata min lokaci."  baya nayi.ina kallonsu har suka bar gidan a hankali na koma ciki, kai tsaye falona na wucce naje na zauna ina tunanin gida gashi babu waya a hannuna.
......
Shiru motar tayi ko kallon inda yake takiyi tsakaninta da Allah take fushi dashi.

"My Queen am so sorry."
"Daddy bani zaka bawa hakuri ba, Aunty ce zaka bawa hakuri kuma kasaya mata waya dan bata da waya tun safe take cewa tayi kewar Ummanta da Mamansu, kuma tana son kiran hajiyarku maganar gaskiya baka kyauta ba, mace ce fa kuma idan da adalci ai bincike ya kamata kafara a gaban kishiyoyinta ka ɗaga hannu ka mareta, kuma tq baka hakuri wallahi in nice bazan baka hakuri ba, nasan ni Yarinya ce amma bazan taɓa barin a cutar dani ba, matukar ina da gskyana."

Shiru yayi yana nazarin maganar Y'arshi. A wani shago suka tsaya ya fita shi da ita, ita ta zaɓar min infinit Hot8 suna gama saya yaje ya saya min layin Mtn, ya saka a laida suka shiga motar,

A gida ya sauketa ya fita ko leka gidan baiyi ba, ya tafi gurinsu Aman.

****

"Wallahi naga makirci kiga fa marinta yayi amma ta nuna a shirye take da wasu hukuncin yarinyar ta iya makirci wallahi in watace kowa sai yasan an taɓa ta."Inji Aneesah.
Taɓe baki fareeda tayi sannan tace.
"Gulma dai ko? Ina makirci anan koda yaran malamai haka suke bazaka taɓa gane ana cutar

dasu ba tsabar an cusa musu munafunci a ransu."

Shigowar Huda yasa suka fashe da dariya " Yar amarya har an korokine."
Banza tayi dasu bata kulasu ba.

........
Daga Gidan Mamie Ahmad ya wucce ofishinsu ya zauna jagwaf, lokacin Aman na waya Rahilah wanda kusan duk hiransu na manyan ne, dakyar ya iya katse kiran.

